BAKAR GABA 1

Kashi na daya 1
Post Suleiman Zidane kd
Whatsapp. 08161272634
littafin Habibullah Muhammad Kabara

BAKAR GABA
PART 1
LBR
HABIBULLAH KBR

rungume suke da juna suna masu kukan rabuwa kamar bazasu daina ba.
inda uban ya dubi dansa mai suna yarim saiman.yace yakai dana bakomai ne yasa boka ulumanu yakeson yakarnuba face tsananin zalunci irin nasa.
saboda haka nake umartarku da kuyi shiri kai da matarka kubar wannan gari ku tafi izuwa kogon darul sihir kuci gaba da rayuwa acan
shidai wannan kogo asalin mallakin wani kasurgumin boka ne.wanda ya kirkiri tsatsuba guda dubu.
saidaya shekara dari yana aikin bokancinsa a ciki sannan ajali ya riskishe tundaga lokacin da ajali ya riskeshi aka rasa mahalukin da zai shiga wannan kogo yafito a raye .
saboda haka nake umartarku da kuyi shiri ku tafi izuwa kogon darul sihir ku ci gaba da rayuwa.
koda yazo nan a zancensa dai hankalin yarima ya dugun zuma.sannan ya dubi yarima yace.bawai inaso ku durfafi kogon darul sihir kai tsaye bane.yanzu haka na hada maka dakaru guda dari wadanda zasu zamo yan rakiya agareka.
sai kuma kuyangi hamsin wadanda zasu kula fa lafiyar gimbiya har zuwa sa'ar da gimbiya zata haihu.
a lokacin ne zata haifi ya mace ko namiji wanda zai zama gagara badau kuma

sadaukin da da'a taba kamarsa kuma
gwarzon mayaki.
a lokadaya cika shekara ashirin aduniya
alokacin ne zai mallaki duk wani sihirin tsafi
da boka awaisul masawi ya bari.kuma
alokacin ne zaku mallaka masa wata takobin
sihiri da zaku dauko.yanzu hakazaku tafi
dajin kurusul saudam domin dauko ita
wannan takobi amfaninta shine komai karfin
sihiri tana iya karya shi.kuma idan tana tare
da kai inzaka shekara kana yaki bazaka gaji
ba.
abu na biyu da zaku samo shine tsumin
dodo harjaju.
shikuma dodo garjaju yanzu haka yana can
wani daji wanda akewa lakabi da dajin ajali.
shi wannan dodo shikadai ya isa ya mallaki
duniya saboda karfin damtsensa dana
sihiri.du wanda yasha。i tsumin dodo garjaju
babu wani kaifi da tsini da zai kara tasiri
ajikinsa da ku
sai kuma abu na uku wanda zaku samo
shine makullin kogon darul sihir wanda
dashine za'a iya bude kofar kogon darul
sihir.
shi kuma wannan makullin ana kiransa da
miftahul sihir.
yanzu haka yana hannun sarkin aljanu na
birni hamshak.
ayanzu haka wadannan aljanu sun mai da
wannan kuba a matsayin abin bautarsu.kuma
akwai tsaro a tattare da ita na sihirtattun
aljanu masu tsnanin karfin damtse.
koda abu saiman yazonan abayaninsa sai ya
dada rungume yarima ajikinsa.sannan a sake
dubansa yace hakika bincike ya tabbatar
mana cewa matarka gimbiya suhaila nada
ciki na wata biyu saboda haka kasan yadda
zakayi ku takaice wannan tafiya acikin wata
goma.
yanzu haka na samar muku yan gudun hijira
mutun dari hudu da kuma kayan guzurinsu.
ba komaine yasa mukayi hakaba face don

asami raguwar kashe kashen da za'ayi a wannan yaki.da kuma burin sake kafa wannan birni sabida haka yaune ranar bakin ciki agareni wacce ban taba tunanin zuwanta ba.
yanzu bada dadewa ba ina mai umartarku daku kama hanya kutafi aikin dake gabanku. nan take kuwa yasa hannu ya bude wata barauniyar hanya dake kusa da gadon mulki. wata katuwar rijiyace wacce akalla sai mutum dubu sun shiga cikinta kuma wani abin mamaki shine acikin wannan rijiya cike yake da haske yadda ko allura ce ta fadi zaka ganta.bude wannan rijiya keda wuya sai sarki abu saiman ya juyo ya dubi yarima yace acikin wannan rijiya zakuyi ta tafiya har tsawon mako guda inda zaku iso wani daji mai tsananin ban tsoro.
da kun iso wannan daji sai ka zare zobenka na sihiri ka cillashi sama to duk hanyar da kaga ya nuna itace hanyar da zata kaiku dajin kurusul saudam sai kubi hanyar.bayan kun dawo daga dajin kurusul saudam sai ka sake cilla zobenka sama.zai sake nuna maka hanyar da zata kaiku dajin ajli.
to haka zaku dinga yi aduk wani abu daya shige muku duhu har ku karasa kogon tsafin boka awaisul masawi.
sannan yaci gaba da cewa da zarar kakama hanyar tafiya karka sake kace zaka sake juyowa ka kalleni don yin hakan kan iya janyo tarwatsewar shirin mu baki daya.
koda yazo nan abyaninsa sai ya daga hannunsa sama ya tafa.
faruwar hakan keda wuya sai ga dakaru guda dari dauke da guziri akan dawakai da kuma kuyangi dauke da ginbiya suhaila.
sai kuma jama'ar gari maza da mata.lokacin da wadannan dakaru da jama'ar garin ramlatul saif suka suka shigo turakar sarki abu saiman sai dukkansu sukayi sujjada agareshi.
sarki ya dubi jama'ar garin yace yaku

jama'ar garin ramlatul saif kuyi sani cewa
yaune zaku fara tafiya mai tsananin hatsari.
saboda haka nake umartarku dakubi duk
wani umarni da yarima saiman zai baku idan
kuka bishi zaku tsira don munaso ku dawo
ku sake kafa wannan birni bayan wasu
shekaru masu zuwa.yana zuwa daidai nan
abayaninsa sai ya taka da kafafunsa yaje
wajen wata akwatin zinareya budeta ya dauko
wani gunki wanda aka kerashi da zallan
zinare.sannan ya juyo ya bawa yarima ya
damka masa ahannunnsa yana mai cewa.
wannan gunkine wanda aka kera mai
siffata.dama nasa an kerashi ne saboda irin
wannan rana.yana zuwa nan azancensa sai
ya sake rungume yarima ajikinsa suna masu
bankwana.
sai bayan dakiku sannan ya sake janye
jikinsa daga jikin yarima idanunsa cike da
hawaye.nan take ya juyawa yarima saiman
baya tare da fadin cewa yanzu haka na
umarceka daka gaggauta kama hanya ka tafi
aikin dake gabanka don cika burin dake
gabannu baki daya.don haka ina gargadinka
kada ka sake juyowa da zummar kallona don
yin hakangangancine a garemu.yana gama
fadin haka sai wani irin hawaye ya zubowa
yarima saboda bakin ciki amma bisa dole ya
kama hanya ya tafi don cika umarnin
mahaifinsa.ma'ana suka shiga cikin wannan
rijiya.
yarima ne a gaba sannan kuyangi,gimbiya
suhaila,mutanen gari.sai dakaru don
tabbabtar da tsaro.
lokacin dasu yarima saiman suka shiga cikin
wannan rijiya sa isarki yajuyo yaje ya sake
rufe wannan rijiya.
WANNAN SHINE ABINDA YA FARU A FADAR
SARKI ABU SAIMAN
a can fadar boka ulumanu kuwa yau yana
cikin farunciki sakamakon binciken da yayi
na rushe birnin ramlatul saif kuma binciken
ya tabbatar masa da samun nasara a

wannan yaki.
dalilin hakanema yasa ya baiwa dakarunsa
hutu na jinsin mutane da aljanu don nuna
farin cikinsa.don hakane ma ya hada walima
afadarsa tsakaninsa da hadimansa.bangaren
aljanu daban na mutane daban.
abisa karaga kuwa boka ulumanu ne ya
zauna bisa karagar mulki yaci ado irin na
manyan bokaye. kai wannan fada ta kawatu da kayan alatu
sosai.hatta iskar da take kadawa acikinta
tatacciyace ba irn wacce aka saba shaka
bace.
bayan yan dakiku kadan boka ulumanu ya
tashi ya fara bayani kamar haka.
yaku hadimaina duk cikinku babu wanda
baisan burina ba.
burin nawa kuwa shine na mallaki na hiyar
nan baki daya.
Adalilin hakane na shiga bincike,kuma
tsafina ya tabbatarmin bazan taba samun
nasara ba.har sai naje na yaki wani birni
wanda ake kira da ramlatul saif na rusheshi
baki dayansa na debe dukiyar kasar.
sannan na shiga dakin bautar su in hallaka
macijiyar da suke bautawa nasha jininta.
da zarar nasha jinin wannan macijiya to
awannan lokacinne duk wani boka dake
nahiyar nan zai dawo karkashina,saboda
babu wanda zai kaini karfin sihiri aduk cikin
wannan nahiyar.
koda yazo daidai nan a zancensa sai ya juya
yayiwa wasu yammata da makada inkiya.
nan take kuwa wadannan yna mata suka
shiga tsakiyar fada suka fara tikar rawa,su
kuwa wadannan makada suka fara kade kade
da bushe bushe.
nan take kuwa fadar ta cika da hayaniyar
mutane da aljanu.
bayan wasu yan dakiku sai wasu kuyangi na
jinsin mutane da aljanu suka fara debo
tulunan giya da kuma kayan abinci suka fara
rabawa hadiman gidan.
koda wadannan hadimai suka ga wannan

abinci sai suka dasa masa wawa hannu baka
hannu kwarya sabo da sun dade basu sami
abinci kamarsa ba.kai wasuma har faduwa
kasa suka dingayi basu saniba saboda
tsananin dadin abincin.
koda boka ulumanu ya lura da abin dake
faruwa sai ya fusata sannan ya dakawa
hadiman nasa tsawa,nan take kowanne ya
dawo cikin hayyacinsa.
sannan yaci gaba da cewa
bawai nataraku bane don ku dinga yin
shashanci ba,nataraku ne don kutayani
farinciki,don haka yanzu zan rubuta wasika
naba daya daga cikinku ya kaita fadar sarki
abu saiman.sanan ya dawo fadata.
nan take boka ulumanu ya bude tafun
hannunsa tare da karanta wadansu
dalasiman tsafi guda uku,yin hakan keda
wuya sai wata farar takarda ta bayyana
ahannunsa,koda bayyanar wannan takarda
sai boka ulumanu ya nuna wani aljani mai
suna markazulu da wannan ta kardar.nan
take wannan takardar t koma hannun wannan
aljani.sannan boka ulumanu yace na
umarceka daka tafi kakaiwa sarki abu
saiman wannan wasika cikin abin da bazai
gaza kwana guda da yini daya ba.
cikin biyayya markazulu yace angama ya
shugabana
nan take ya bude fuka fukansa ya luluka
cikin srarin samaniya cikin azababben gudu
tamkar tauraruwa mai wutsiya
WANNAN SHINE ABIDAYA FARU AFADAR
BOKA ULUMANU
al'amarin yarima saiman kuwa tun lokacin da
suka bar birnin ramlatul saif ta cikin wannan
rijiya sai suka wanzu suna tafiya cikin
karkashin kasa har suka isa bakin wannan
rijiya.
sai ganinsu sukayi cikin wani makeken daji
mai ban tsoro.
daga bayan wannan rijiya kuma wasu
ingarmun dawakai ne sunata faman harbin

iska.
koda su yarima suka tsinci kansu awannan daji duksai suka ji wani tsoro ya darsu a zuciyarsu..yarima saiman ne kadai hankainsa bai tashi ba,kai tsaye ya durfafi inda wadannnan dawakai suke ya zabi daya ya mikawa gimbiya suhaila sannan ya umarci dakarunsa suje su zabi nasu dawakan.nan take suka je babu hayaniya kowa ya zabi guda daya ya hau.
bayan kowanne badakare ya hau nasa dokin sai yarima saiman ya umarci jama'ar gari da suma suje su hau nasu dawakan.
batare da bata lokaciba suma sukaje suka cika umarni.saida kowa ya zabi nasa dokin sannnan shima yaje ya zabi nasa dokin yahau sanna ya zaburi dokin zuwa gabashin dajin batare da sanin inda ya nufaba.
nan da nan suma dakarun suka saki linzaman dawakansu suka bi bayansa cikin tsananin gudu mai tada hankali.
hakika alokacin da yarima saiman kejan wannan zuga tasa duk irin halittar da tai karo dashi a wanna lokaci to kwananta ya kare
WANNAN SHINE ABINDA YA FARU GASU YARIMA SAIMAN BAYAN SUN BARO BIRNIN RAMLATUL SAIF
Al'amarin aljani markazulu kuwa bayan ya baro fadar boka ulumanu da nufin kai sako izuwa fadar sarki abu saiman
sai ya wanzu yana mai tsala azababben gudu nagaban kwatance har sa'a uku ta shude.
kwatsam ba zato ba tsammani sai yaci karo da wani murgujejen dodo mai tsananin muni.
kafin markazulu yayi wani yunkuri tuni dodon yasa hannu ya makoshi kasa.
nan take kuwa markazulu ya fadi kasa sumamme.
koda faduwar markazulu kasa sai wannan dodo yasa hannu ya dauki markazulu ya dorashi akafadarsa sannan ya nufi wani kogon dutse dake tsakiyar dajin cijin

tsananin farinciki domin yau shekararsa uku
rabon dayaci naman aljani,naman mutane
kuwa shekararsa goma sha biyar kullum sai
dai yaci naman dabbobi. Lokacin da dodon ya iso bakin kogon nasa
sIai ya kwankwasa wata kofa ta bakin
karfe,ita dai wannan kofa an sana'anta tane
da zallan bakin karfe,
fadin ya kai kamu hamsin tsawon kuwa yakai
kamu talatin.
amma bisa mamaki sai wata yar karamar
yarinya ta leko ta wata yar karamar taga.
koda taga mahaifinta ya dawo da wani
murgujejen aljani akafadar sa sai rugo da
gudu tazo ta budewa mahaifin nata kofa
tamkar yadda zaka janye murfi daga jikin
tulu.
nan take wata kara mara dadin ji ta cika
dajin baki daya sakamakon bude wannan
kofa.
ba tare da bata lokaci ba wannan shid
ge cikin kogon ya jwo wani kejin bakin karfe
ya jefa aljani markazulu ciki ya rufe
sannan ya juyo ya dubi yarsa yace
yake yata mafi soyuwa agareni ki sani cewa
yau nayo farautar da ban taba yin kamarta
ba
domin wannan aljani yana dag cikin manyan
dakarun boka ulumanu wanda ya kashe miki
mahaifiyar ki a shekarun da suka gabata
kuma ina mai yi miki albishir cewa kece da
kanki zaki kashe wannan aljani kisa mafi
munin da mukewa halittun da ke doron kasa
yadda zamu kunsawa boka ulumanu bakin
cikin da bazai taba mantawa da shiba
lokacin da dodo shrmanu yazo nan a
zancensa
sai yarsa samriya ta bushe da dariya har
zuwa wasu lokuta sannan tace ya abbana
hakika yau kacikan babbab burina koda ban
kashe boka ulumanu ba
sa'ad da samriya tazo nan a zancenta sai ta
mike tsaye cike da farinciki ta shige wani
daki dake cikin kogon ta kwanta.

kwanciyar samriya keda wuya sai barci ya dauketa.
sannan shima dodo sarmanu ya tafi shima ya sami guri ya kwanta nasa barcin don huce gajiyw
kash hakika rashin sani ya fi dare duhu inda dodo sarmanu ya san abinda zai faru da baiyi gangacin kwanciya barciba domin ya manta bai dauke makullin kejin dayasa aljani markazulu a ciki ba.kwanciyasa jeda wuya sai wani hadari mai karfi ya ta
so nan take aka tsuge da ruwan sama kamar da bakin kwarya.
da ike kejin da aljani markazulu yake ciki yana daga bakin tagar kogon sai nantake aljani markazulu ya farfado daga dogon suman da yayi sakamakon ruwan da yake shigow ta cikin tagar
lokacin da markazulu ya farfado daga dogon suman da yayi kuma ya ganshi cikin keji sai ya cika da tsananin bakin ciki akan abu biyu.
abu na farko shine bai taba tunanin akwai wani acikin duniya da zai iya yi masa irin wannan kamu ba kamr dabba
abu na biyu kuma shine mai zai cewa boka ulumanu idan ya koma can fadarsa alhlin sunyi alkawarin zai kai wannan acikin kwna guda da yini daya.
koda ya gama wannan tunani sai ya sake cika da bakin ciki mara misaltuwa.
kwatsam ba zato ba tsammani sai yayi kicibus da kubar wannan keji da yake ciki koda yaga wannan kuba sai y sake jin murna t akama shi har ta disa sar da bakin cikin da yake ciki.
ba tare d bata lokaciba kuwa ya zuro hannu ya dauki wannan kuba ya zura ta a cikin gidanta sannan sannan ya murda nan take kuwa wannan kofa ta bude.
nan take marlazulu ya fito daga cikin kejin da yake ciki sannan ya zare takobi ya nufi kan dodo sarmanu kai tsaye ba tare da fargababa ya daga takobin ya caka masa ita

acikin ido
nan take kuwa dodo sarmanu ya kwalla uban ihu
wanda yayi sanadiyar farkawar samriya daga barci
koda taji karar mahaifinta sai tayi tsalle ta zare wata sharbebiyar takibi dake jikin bangon kogon ta rugo dq gudu izuwa inda mahaifinta ke kwance kwatsam sai taci karo da gawar mahifinta kwance cikin jini ga kuma bakon aljanin da suka kamo rike da takobi tana yoyon jini.sai ranta yayi matukar tashi
nan take ta falfalo da azababben gudu tana mai kwarara uban ihu koda tazo daf da markazulu da nufin tai masa kwaf daya sai aljani markazulu yayi tsalle ya tsallake harin nata nan take aka ruguntsume da azababben yaki na gaban kwtance tsakanin markazulu da samriya
wohoho hakika fadan manyan dawa yayiwa yara nisa domin ana fara wannan yaki samriya ta toshewa markazulu kofofin tsira amma saboda tsananin bakin naci irin na markazulu sai yaki yarda yaje kasa
Azahirin gaskiya samriya tafi aljani markazulu karfin damtse shi kuma markazulu yafita juriya naci da iya yaki.
samriya ta wanzu tana mai kaiwa markazulu sara da suka ta ko ina.
shi kuma ya wanzu yana mai kare saran nata cikin zafin nama.sai da suka sahafe lokuta suna wannan fada kowaya kasa samun nasara akan dan uwan fadansa bisa dole dukkansu suka ja da baya suna masu hararar juna kamar zakaru.
daga can sai samriya ta dubi aljani marjazulu tace
yakai wannan la'anannen aljani kayi sani cewa yau ka tsokanowa kanka bala'in da ba zaka iya fita ba domin mahaifina daka kashe shine dan autan sarkin dodannin duniya wato dodo garjaju

wanda yanzu haka yana can dajin ajali don
na tabbata yanzu yasan ka kashe dansa
don haka akoda yaushe zai iya turo yan
uwan mahaifina domin daukar fansa akanka .
koda samriya tazo nan a zancenta sai
markazulu ya bushe da dariya sannan yace
ke yarinya ki sai wanda ya rigaka kwana dole
ya rigaka tashi domin ni da kike ganina na
girmi mahifinki nesa ba kusaba don haka
koda yaushe ashirye nake dayin mugun gamo
ni da yanuwan mahaifinki
koda yazo nan abayaninsa sai ya shammaci
samriya ya cilla mata wata allurar sihiri
nan take kuwa samriya ta fAdi kasa ma
tacciya
faruwar hakan keda wuya sai aljani
markazulu ya sake bushewa dadariya akaro
na biyu sannan ya durfafi kofar kofar fita
daga kogon don ya budeta ya fita.
koda ya kai hannu da nufin budeta sai yaji
tamkar zai dauki duniya saboda tsananin
nauyi bisa dole ya saki kofar kogon cikin
tsananin ta shin hankalidomin yasan indai
yace zai zauna aciki wannan kogo bazai
dadeba zai mutu

LITTAFIN
BAKAR GABA
PART 2
TYPING HABIBULLAH KBR
Amma sai ya yanke hukuncin yakoma cikin
kogon kozaiga makullin kofar kogon.
nan take kuwa ya nausa cikin kogon batare
da sanin inda ya dosa ba.saida ya wuce yan
dakiku yana shige da fuce acikin kogon
sannan ya ido wani daki mai dauke da kayan
tsafi iri iri.koda isowar markazulu bakin
wannan daki sai ya cika fa farincikidomin
yasan cewa tabbas zai sami abinda zai
taimakeshi ya fita daga wannan kogo acikin
wannan daki.
nan take yashiga cikin dakin ya hau lalube

baji ba gani
kwatsam sai yaci karo da wani gurun tsafi acikin wata battar karfe mai dauke da ruwa aciki.
Al'amarin dayasa aljani markazulu cikin tsananin mamaki kenan kuma yji tsoro ya darsu azuciyarsa
amma daya tuna cewa yana cikin halin rai da mutuwa,
ma'ana ko sa'a ko kishiyarta kawai sai yaji ya daina jin tsoron komai acikin zuciyarsa
nan take kuwa yasa hannu ya zaro gurun tsafi daga cikn battar ya zura shi ajikin hannunsa na hagu
sanna ya daga battar ya zura a bakinsa ya shanye ruwan da yake ciki.
nan take kuwa yaji wani gagarumin karfi ya shiga jikinsa wanda bai tabajin kamarsa ba tamkar zai iya nada gammo ya dauki duniya gaba dayanta.
koda aljani markazulu yaji sauyin yanayi ajikinsa sai yayanke hukuncin ya debe ragowar kayan tsafin gaba dayansu.bayan ya kwashe kayan tsafin ne sai kuma sai ya juya ya nufi kofar fita daga kogon
koda aljani markazulu ya iso bakin kofar kogon sai yasa hannu ya bude kofar kogon tamkar yadda shaho yake daukar dan tsako sannan ya fita daga kogon.
koda markazulu ya fito daga kogon sai ya cika da tsananin farin ciki don ganin ya tsira d rayuwarsa bai halaka ba aciki.
sannan kuma yaji wani irin girman kai ya shiga jikinsa.
nan take kuwa ya daga kansa sama ya fara yiwa kansa kirari yana cewa
saini hadari malafar duniya
ayaune nacika sunana markazulu kuma ayaune zan addabi duk wani abu mai rai dake doron kasa.
kuma daga yau nafi karfin nayi bauta ga kowanne bil'adama dake doron kasa,ballantana ulumanu kaskantaccen boka.

sai ni rugugin bala'i
saini rijiya gaba dubu
saini gobara daga kogi
koda yazo daidai nan a kirarinsa sai ya bude
fuka fukansa ya tashi sama ya luluka acikin
gajimare.
++ ++ ++ ++ ++
wanna shine abindaya faru a kogon dodo
sarmanu da aljani markazulu
++ ++ +n+ ++ ++
a can fadar boka ulumanu kuwa yaga duk
abindaya faru ga aljani markazulu da dodo
sarmanu
da irn bakaken magan ganun daya fada
masa.saboda haka sai yaji ya tsani
markazulu saboda bakaken magan ganun
daya fada masa
da kuma asarar babban hadiminsa da yayi
wanda ya yarda dashi.
tabbas yasan cewa yanzu baida karfin sihirin
da zai yaki markaulu yanzu
saboda sihirin da yake cikin battar karfen
dodo sarmanu sihirine mai karfin gaske.
don haka sai boka ulumanu ya yanke
hukuncin sai bayan ya gama mamaye
nahiyar da karfin sihirinsa dana sarauta
sannan zai kama aljani markazulu yayita
gana masa azaba har sai ya mutu
nan take ulumanu ya tashi wani hadimin
aljaninsa ya bashi wata wasikar yaki ya
aikashi ya kaiwa sarki abu saiman.
nan take aljanin ya cika umarni bayan kwana
daya aljanin ya fawo da wasikar raddi ya
mikawa boka ulumanu.
cikin kankanin lokaci baka ulumanu ya fara
hada rundunar yakai ta gaban kwatance kai
kace duniya zasu yaka.
bayan kowanne badakare ya hallara sai boka
ulumanu ya daga hannunsa sama yana mai
nuni da kowa yayi shiru
nan take kuwa gurin yayi tsit kamar mutuwa
ce ta gifta bayan shudewar wasu yan lokuta
sai ya soma jawabi kamar hak.

yaku daukacin hadimaina kuyi sani ayanzu
zanfara shirin yakin daban tabayin kamarsa
ba atarihin rayuwata.
saboda haka ubangiji na ya umarceni na fada
muku cewa ni zan barku anan kuyita baiwa
kanku horon yaki na tsawon wata guda
nikuma zanje kudancin birnin kisra domin na
samo wani wanda zai iya kashe macijiyar da
birnin zaharul maswur suke bautawa
amatsayin ubangijinsu..amma idan d mai
tambaya sai yayi.
nan take kuwa wani hadimi yada ga
hannunsa sama alamar yana da tambaya.
sai boka ulumanu ya bashi umarnin yayi
tamabayar.
sai wannan badakare yce ya shugabana
tambaya itace menene abin dogaron shi
wanna aljani da zai iya yaki da abar bautar
sarki abu saiman?
da jin wannan tambaya sai boka ulumanu ya
bushe da dariya sannan yace
yakai marwan kayi sani cewa
shidai wannan aljanj ana kiransa da suna
harisula mar'uf
kuma baya dogaro da wani karfin sihiri sai
wata takobi da yake da ita itace kadai abr
dogaronsa.
sannana kuma yanada matukar karfin
damtse.
don a yanzu babu alanin daya kaishi karfin
damtse da iya yaki a duk fadin duniyar nan
yazu haka harisul maruf yayi rantsuwa akan
bazai sake aiki a karkashi kowanne mutumba
face wanda ya dawowa da mahaifiyarsa
ainihin siffarta daga siffar gunki zuwa ainihin
kamarta
kuma aduk duniy ni kadaine nakeda sihirin d
zan iya wannan aiki. Koda boka ulumanu yazo nan a zancensa
sai wani aljani mai suna arman yace
ya shugaba na muna so muji tarihin harisu
maruf dakuma gwagwarmayar dayasha a
rayuwarsa
dajin haka sai boka ulumanu yabushe da

dariaya sannan yace hakika kunyi mini
tambaya mai matukar mahimmanci don haka
zanyi kokarin takaice muku tarihin shi
wannan sadaukin aljani.
nan take ya soma labari kamar haka
a wasu shekaru da suka gabata a can
kudancin birnin kisra anyi waji sadaukin
aljani mai tsananin karfin damtse wanda
duniyar sadaukai ta yadda dashi
shi dai wannan aljani ana kiransa da suna
harisul mar'uf
wata rana harisul ya tafi tarauta don samo
abinda zasuci shida mahaifiyarsa.
koda ya dawo gida sai yayi bakin gamo da
abinda ya tsana aduniya.
bakomai ya gani ba face mahaifiyarsa mai
suna zumaira a kwance akasa kafafunta a
nan nade da alama ta zama gurguwa.
nan take harisul mar'uf ya ruga da gudu
gareta ya dauketa ya dorata akan gadonta na
itatuwa.
sannan ya dubeta yace yake ummina ki
gaggauta fadamini abindaya sameki bayan
tafiyata faruta.
koda aljana zumaira taji wannan tambaya
daga bakin danta aljani harisul mar'uf sai
aljana zumaira tace
yakai dana bayan tafiyarka sai na wanzu ina
mai zaman jiran dawowar ka a wannan waje.
ina cikin wannan haline kwatsam sai naga
wannan gida da nake ciki ya soma girgiza da
kuma wani irin jan hayaki.
wanda bansan ta inda yake shigowaba
ina cikin wannan haline kawai sai naje
kafafuna sun soma nan nadewa.harsaida
suka zuke suka koma kanana.yadda bazan
iya taka suba.
koda tazonan a zancenta sai ta dada
fashewa da kuka.
lokacin da harisul mar'uf yaji bayanin
mahaifiarasa sai sai nan take ya rungumeta
akirjinsa tare da fashewa da wani sabon
kukan.

daga can kuma sai ya janye jikinsa daga
nata sannan yace
yake ummi na nayi rantsuwa da wannan
hawye naki duk wuya duk rintsi sai na samo
miki maganin wannan lalura duk wuya duk
rintsi.
kuma sai na hallaka duk wanda nagano dasa
hannunsa acikin wannan aiki.
nan take harisul Mar'uf ya bde fuka fukansa
ya nausa cikin daji don samowa
mahaifiyarsa duk wani kayan amfani da zata
bukata na tsawon shekaru dari uku.
sannan yayi sallama da mahaifiyarsa ya tafi
wajen wani amintaccen bokansa.
sai da yayi tafiya sa'a bakwai sannan ya isa
bakin kogon garmanu nan take ya saki fuka
fukansa ya sauka bisa turba.
saukarsa keda wuya sai ya cika da mamaki
bakomai yaganiba face boka garmanu
fuskarsa cike da fara'a.
nan take ya fara yiwa harisul mar'uf kirari
yana cewa
lale marhaban da sadaukin duniya tarwatsa
maza.
ajali kake bakasan hakuriba
dodo kake mai razana manyan sadaukai
duhu kake mai firgita manyan maza afilin
daga
kabari kake makomar duk wani mahaluki
ya sarkin sadaukan duniya.
lokacinda boka garmanu yazo nan a
kirarinsa
sai yace da harisul mar'uf
yakai sadaukin zamani kasani cewa
bakowane yayi mahaifiyarka wannan sihiriba
face sarkin bokayen duniya.
wato boka salban sakamakon binciken da
yayi a cikin tsafinsa ya nunamai cewa kai
kadaine saka iya zame masa matsala acikin
al'amuran da yake guda narwa a doron
kasa.har kayi yunkurin hanashi
saboda hakane yakara tsananta bicike a
madubin tsafinsa daga karshe yagano cewa

dolene ka shiga sha'anin zaluncinsa
muddinsa muddin bai zaunarda mahaifiayrka
awaje dayaba.
ma'ana ya aika mata da sihirin da zata daina
tafiya baki daya.
koda boka garmana yanzo nan a zancensa.
sai harisul mar'uf yace.
to yanzu a ina zansami boka salban na
hallakashi don nadauki fansar abinda ya yi
mini?
dajin wannan tanbaya sai boka garmana ya
bushe da dariya kamar bazai daina ba.
dagachan kuma saiya tsuke bakinsa kamar
an aiko masa da sakon mutuwa.
sannan yace
yakai gwarzon shekara mahaifiyarka bazata
taba samun lafiya ba hsar sai kaje kowanne
bakgare na duniya ka samo mata wasu
tsumummuka ka hada su waje daya ka bata
tasha sannan zata sami lafiya kamar babu
abindaya sameta.
sai kaje ka samo wadannan abubuwa sannan
zakayi shirin tunkarar boka salban
kodajin haka sai harisul mar'uf ya ta karkare
ya kwarara uban ihu
yace narantse da darajar hawayen
mahaifiyata saina samo mata wadannan
tsumummuka koda zan rasa rayuwata
sannan na yanko kan boka salban na tsireshi
atsakiyar birnin da yafi kowanne birni yawan
matsafa don hakan ya zamo gargadi
agaresu.
dajin haka sai boka garman yace
ina da wani taikako da nakeson baka na
wani sihiri mai karfin gaske wanda zai
kareka dga dukkan wani hatsari da tsautsayi.
sai harisul mar'uf yayi murmushi ga boka
garmana
sannan yace
ina da takobin da indai ina tare da ita zata
dinga bani kariya.don haka daga yau abzamu
sake haduwa ba ni dakai sai ranar da naje
na samo wannan magani.

kuka daga yau mun kulla bakar gaba da
boka salban.
koda gama fadin haka saiya bude fuka
fukansa ya tashisama ya luka acikin
gajimare cikin azababben gudu na gaban
kwatamce.
duk inda ya gifta ya tarar da wani ayari na
aljanu da sun ganshi saidai kaga sun chanja
hanya saboda tsananin kwarjiinsa.
idan kuwa tarom yan fashine cikin kankanin
lokaci yake tarwatsasu.
sai daya shafe kwanaki bakwai yana tafiya
sannan ya iso bakin wani birni na aljanu don
haka ya yanke shawarar ya shiga wannan
gari ya kwana idan gari ya waye sai ya kama
hanya ya cigaba da tafiyarsa.
nan take kuwa ya sauka abakin kofar wannan
kasa sannan ya matsa gaban kofar ya
kwankwasa.
bisa mamaki sai wani aljani ya leko yan
cewa wannan wanne me karar kwanane yake
bugu mana kofa alokacin da muke morewa
da kyawawan matanmu?kowanene ya
gaggauta juyawa da baya tun kafin fishina ya
sauka akansa.
koda wanna me tsaron kofa yazo nan a
zancensa sai ran aljani harisul mar'uf ya
baci.amma saiya basar yace nine harisul
maruf wanda yake neman mutuwa da
kudinsa kuma akoda yaushe.
dajin haka sai ran mai tsaron kofa ya baci.
nan takekuwa ya bude kofar wannan kasa.
sai dakaru sukayita fitowa da makamai iri iri
tamkar duniyar zasu yaka.
bayan wadannan dakaru sun gama zagaye
harisul maruf sai sukayi kukan kur suka afka
masa da sara da suka.cikin tsananin zafin
nama d ajuriya da bajinta nan take aljani
harisul mar'uf ya shiga kai sara da suka
cikin salo irin an manyanyan jarumai.
cikin kankanin lokaci ya karar dasu ya
zamana saura shugabansu.
nan take kuwa shugaban masu tsaron kofar

ya ruga aguje domin ya fadawa sarki
abindaya faru.
tafiyar keda wuya sai sai harisul maruf ya
matsa gaban kofar wannan birni wacce
takeda girma sosai.idan ta fadi sai an sami
manyan giwaye guda dari biyar sannan zasu
iya dagata.yasa kafarsa ya doki kofar.
nan take kuwa wannan kofar ta rufta ciki.
kuma adai dai wannan lokacin ne sarkin
wanna garin ya iso.
koda yaga abindaya faru sai ya kwarara uban
ihu. Koda yaga irin muguwr barnar da yayi masa
sai ransa yayi matukar baci tare d kwalla
ihu.
domin bincike ya tabbatar da cewa aduk
lokacin d wani sadauki ya balla wannan
kofar to daga ranar to daga bashi ba mulki
acikin kasar harsai ya nemi hadin kan
wannan sadauki sun tari masifar d zata afko
musu.
nan take kuwa ragazalu yasa hannu ya
finciko sarkin kofa sannan ya dubeshi yace
ka jawo mana bala'in da bamu taba
shigaba,tundaga sanda aka kafa wannan
kasa,tunda ka janyo mana sadaukin aljanun
duniya harisul mar'uf,don haka hukuncinka
shine kisa.
nan take yasa takobi ya datse masa
kai,sannan yayi wurgi da gawar,tare da bawa
dakarubsa umarnin suyi mubaya'a ga harisul
maruf
nan take dakarun suka cika umarni
sannan sarkin ragazalu ya tao da kafafunsa
yazo gaban harisul maruf yayi mubaya'a tare
da fadin
kagafarceni ya sadukin duniya bisa irin
tozartar da akayi maka acikin kasata.
bakomai ya jawo hakaba face tsaurin ido rin
na sarkin kofa,
yakai wannan babban jarumi dagani har
jama'ata mun mika wuya agareka,kuma
muna neman taimakonka sakamakon karya
alakadarin kasarmu dakayi na balla mana

kofa,
kuma bincike ya nuna cewa daga lokacin da aka balla wannan kofa zaman lafiya zai kare a wannan nahiya,sakamakon kawo mana farmaki da kasashen ahokan gaba zasu dingayi badon komaiba sai don su mallaki dukiyarmu ta dangin zinare da lu'u lu'u yanzu haka.maganar da nake maka wasu kasashen sun fara shirin kawo mana mamayar bazato yau ko gobe.
lokacin da sarki ragazalu yazo nan azancnsa sai ya fashe da kuka,
al'amarin da yasa zuciyar harisul mar'uf tayi sanyi kenan don haka sai yadubi sarki ragazalu yace
yakai wannan adalin sarki zan taimakeku,saboda banason ganin anzubarda jinin wanda baijiba bai ganiba.
don haka nayi alkawarin taimakon mayakanku,don haka yanzu sai kuyi shirin
Suleiman Zidane kd
Whatsapp. 08161272634

gyara kofar wannan gari tun kafin abokan gaba su cimmaku.
koda sarki ragazalu yaji haka saiya kamu da tsananin farinciki sannan ya umarci wani badakare da yaje yayi shelar ana neman duk wani magini da yake cikin kasar da ya hallara abakin kofar wannan birni
nan take kuwa wannan badakare angama ya shugabana sannan ya bace.
kafin cikar.sa'a biyu duk wani magini ya hallara
sannan sarki ya basu umarnin fara gini
kafin cikarsa'a bakwai sungama gini wannan kofa
sannan aka aka dada kara dakarun tsaro ako ina acikin garin aka cigaba da jiran ta inda dakarun zasu bullo
a.haka.suka.kasance cikin shigar yaki taban tsoro.

saida suka shafe yini guda sannan abokan gaba suka iso.
awannan rana anyi gagarumin yakin da ba'ataba kamrsaba awannan nahiya.sannan anyi asarar dukiya mai tarin yawa.
bisa dole kowanne bangare yajanye dakarunsa gaba daya.
tundaga wannan rana kasashen dake duniya suke matukar tsoron wannan birni saboda arin sa'ar da suka samu awannan yaki.
a zatonsu har yanzu harisul mar'uf yana cikin kasar.
wash gari kuwa da sassafe harisul mar'uf yatashi yabar kasar bayan sunyi sallama da sarkin garin da yan majalisarsa.
sannan yanausa cikin gabashin duniya don nemowa mahaifiyarsa magani,
sai da yayi tafiyar shekara guda sannan ya iso dajin da yake dagashi sai bangon duniya.na gabas
saboda haka sai harisul mar'uf ya zaro sihirtacciyar takobinsa dake daure a kugunsa.
sannan ya zaro wata yar taswira wacce ya samu agurin sarki ragazalu
yabudeta ya duba.
nantake yayi arba da wani kogo acikin taswirar,wanda yake nuni da shine hanyar da zata kaika bangon duniya nagabas.
nantake kuwayasake bude fukafukansa yana mai kusantar kogon kai tsaye.
yana shiga cikin kogon sai yayi arba da wata yar siririyar hanya wacce take da tsananin nisa.
nantake kuwa ya nufi wannan hanyar kai tsaye yana mai gyara rukon takobinsa.
kwatsam sai yayi arba d wata bakar kunama wacce ta tokare hanyar kogon gaba daya.sannan wannan kunamar tasa kafa ta daki wani dutse da kafarta guda daya
nantake kuwa wannan dutse ya gangara yaje ya toshe hanyar da harisul maruf ya shigo.
mai makon ma harisul mar'uf ya firgita

sai abin ya bashi mamaki don ganin irin wannan azababben karfi irin na wannan kumama.
bakomai yabashi mamakiba face gani yadda ta iya ture wannan dutse da kafarta daya.
alhalin inza'a tara manyan aljnu guda ashirin bazasu iya mirgina wannan dutseba.
yana cikin wannan tunanine yaji kunamar takawo masa harin bazato.
cikin tsananin zafin nama ya daka tsalle ya koma gefe daya don ya soma tunanin ta hanyar dazai bullu mata.
nanfa aka soma kallon kallo tsakanin sa da wannan kunamar na tsawon yan dakiku.daga chan sai harisul mar'uf ya nufi kunamar cikin mugun nufi,
suna haduwa aka ruguntsume da masifaffen yaki nagaban kwatance suka wanzu suna masu kaiwa junansu sara da suka.
shidai yana amfanine da takobin sihirinsa ita kuma tana amfanine karinta da kuma hannayenta wajen kai masa hari.
duk sa adda harisul maruf ya sari jikin kunamar sai sai yaji kamr dutse ya sara.
ita kuma kunamar duk sanda ta kawo masa hari ya kauce duk abindata samu nan take yake ruburbushewa ko kuma ta haddasa wawakeken rami.
sai da suka shafe sa'a guda suna fafatawa,sannan kunamar ta sami nasarar yankan harisul mar'uf agadon bayansa.
nantake harisul mar'uf ya kwalla ihu.saboda zafi da zugin da yaji.cikin tsananin dauriya ya daka tsalle tsalle kamar daga cikim baka aka wullashi ya fada kan gadon bayan kunamar sannan ya caka mata takobi a ido.
nan take kuwa idon kunamar ya fashe jini yayi tsar tuwa.nantake kunamar ta haukace ta dinga kawo masa mugayen hare hare
LIKE AND COMMENTS IS OUR ENCOURAGEME (IBNI ABDULLAHI ABDULLAHI)
LITTAFIN BAKAR GABA PART 3
LBR
HABIBULLAH KBR

TYPING HABIBULLAH KBR
Suleiman Zidane kd
Whatsapp. 08161272634

nan fa wannan fada ya dawo sabo kogon ya soma girgiza tamkar zai ruguje.
cikin dan kankanin lokaci aljani harisul a fita daga hayyacinsa saboda tsananin wahalar da yakesha awajen kunamar.
saidaya zamana yakasa maidawa kunamar da martani saidai yunuri kare kansa kawai yakeyi.
koda aka shafe wata sa gudar sannan harisul mar'uf yasami nasarar cakawa kunamar takobi atsakiyar wuyanta.
nantake kunamar tafadi kasa ko shurawa batayi ba.
sannan shima ya fadi kasa sumamme.
sai bayan sa'a uku sannan ya farfado daga suman da yayi.
yana farfadowa ya tuna da ciwon dake gadon bayansa
nantake yadauko magani daga cikin jakar guzurinsa.yazuba aciwon dayake bayansa.sannan ya tashi yagyara damararsa ya nufi hanyar da zata fitar dashi daga wannan kogo,sai bayan yan dakiku sannan yafita daga cikin kogon.
yana fita yayi arba da wani tafkeken daji mai matukar kwarjini daban tsoro,
shidai wannan daji yakasance babban daji mai dauke da ababan tsoro,
don hatta bishiyoyin dajin siffofin dodanni ne dasu,
kuma awannan lokaci rana ta bude.hakanne ya haddasa wata iriyar zazzafar iska acikin wannan daji.
duk haka baisa harisul mar'uf tsoroba ya dada kutsa kansa cikin dajin cikin azabbaben gudu acikin sararin samaniya da nufin ya wuce ta saman dajin.
kwatsam sai yaji tamkar an ruke fuka fukansa yadda bazai iya motsa suba.

bisa dole yaci burki asama don yaga abin da zai faru.
yanacikin wannan haline yaji wata kakkarfar iska ta zukoshi kasan wannan dajin.
alokacinda wannan iska ta sauke harisul mar'uf akasan wannan dajin.
kwatsam sai yayi arba da wasu manya manyan macizai masu matukar ban tsoro.
sudai wadannan macizai adadinsu yakai dubu daya.haka girman kowannensu yakai giman bishiyar dabino haka kaurinsu yakai bishiyar kuka.
idanunsu kuwa tamkar angasa dan buda a wuta.
alokacin da wadannan macizai sukaga harisul mar'uf asararin samaniya sai suka bace tamkar basu taba wanzuwa ba,sannan itama wannan iskar ta dauke tamkar bata taba samuwaba.
kuma alokacin ne harisul mar'uf ya daina ganin macizan.
al'amarin daya matukar bashi mamaki kenan sannan ya fara tunanin irin masifar da take cikin wannan dajin,domin yasan ta hanyar dazai bullu musu.
gashi kuma azahiri yaga halittu agun amma yanzu kuma yaga basa wajen yanzu.
nan take azuciyarsa kawai ya shiga dajin kai tsaye,amma ya dinga kula da motsin kowacce irin halitta ya gani.
sannan ya zaro takobinsa ya kutsa kansa batare da fargaba ba.
awannan lokaci rana ta bude tamkar zata gasa masa kansa.
sai dayaje tsakiyar dajin sannan kasa ta fara tsagewa tamkar zai rufta cikinta,bishiyoyi suka soka karyewa,duwatsu suka dinga mirginawa.
kwatsam sai harisul mar'uf yayi arba da wadannan macizai suna saka shi atsakiya yadda babu wanyar da zai iya wucewa.
daya daga cikin macizan ya sari wani dutse dake kusa dashi,nantake dutsen ya rbe gid

biyu wata bakar kumfa tayi tsartuwa daga
bakin macijin.
alokacin da wannan abu ya faru harisul
mar'uf yana tsaye yana kallon ikon allah.
kwatsam sai wadannan macizai suka taso
masa da harbi suna wani irin kuka mara
dadinji.
nantake aka ruguntsume da azababben yaki
nagaban kwatance yana zamana suna masu
kaiwa juna sara da amakamansu.
shidai harisul mar'uf yana amfni da
takobinsa.
su kuma suna kai masa harin da bakinsu
dakuma jelarsu,wajen kai masa sara,
nanfa guri ya rincabe da hucin macizai
saboda tsananin bala'i,
cikin kankanin loakci suka hargitsa dajin da
buge buge.
duk sa'ar da suka kawo masa duka ya kauce
duk abinda suka samu nan take yake
ruburbushewa,
idan sara suka kawo masa da bakinsu idan
ya kauce suka sami kasa,nan take suke
haddasa wawakeken rami mai zurfin gaba
biyar.
shikuwa harisul' maruf saran macizan yake
baji ba gani.wani lokacin idan ya daki daya
daga cikinsu sai kaga kamar an janshi da
majaujawa,duk da irin wannan girma nasu,
hakika jarumataka baiwace duka wanda allah
ya bawa ita ya dace kaduba girma irin na
wadannan halitttu amma sai gashi aljani
guda daya yana neman rinjayarsu.
lokacin da gumurzu yakai gumurzu sai
macizan suka fuskanci nasarar da yake
samu akansu sai duk gaba dayansu suka ja
da baya suka tsaya ana kallon kallo
atsakaninsu.
shidai harisul mar'uf game da wadannan
macizai shine.
dukda yana samun damar saransu da
sukarsu amma daya daga cikinsu yaki ya
mutu saboda tsananin taurin eansu.

sukuma macizan shine
suna tunanin hamyar da zasubi su hallakashi
cikin sauki batare daya sami nasarar hallaka
daha daga cikinsu ba.
nantake kamar hadin baki suka sake afkawa
kan juna da azabben yaki wanda yafi na
farko.
awannan lokacin suaknsu macizan sai suka
chanza salon fada suna masu kai da kansu
da jelarsu lokaci guda.
duk sa'adda ya kauce duk abinda suka samu
nan take yake ruburbushewa ya zama kamar
gari.
ana cikin hakane wani maciji mai matukar
sa'a ya shammaci harisul mar'uf ya gabza
masa jelarsa agadon baya,
saboda tsananin karfin dukan sai da harisul
mar'uf yayi sama ya gwaru da jikin wani
katon tsauni.
nan take wani gudan jini yayi fitar burgu
daga bakinsa,sannan yaji gaba daya jikinsa
yadau zafi. ya mike tsaye tare da gyara tsayuwaarsa.
nan take ya sake rugawa izuwa kan
wadannan macizai,cikin mugun nufi yana mai
karaji da kuwwa yana mai kai sara da suka
cikin tsananin zafin nama,juriya da bajinta
fiye da farko.
a wannan lokaci sai ya canja salon yaki ya
koma kai sara a tsakiyar makwallaton wuyan
macizan,cikin sa'a kuwa wadannan macizai
suka fara halaka,ihun su da rurinsu ha cika
dajin baki daya.
babu abinda zai baka mamaki face ganin
yadda harisul mar'uf yake hallaka wadannan
macizai farat daya.
wani lokacin ma har tsalle zakaga yanayi
akan kawunansu yana wasa da hankalinsu.
cikin kankanin lokaci yagama hallakar dasu
baki dayansu.
sannan ya tashi ya bude fukafukansa ya
luluka acikin sararin samaniya,yanufi
hanyarda zata kaishi karshen dajin.
sai da yayi tafiyar sa'a biyu,

sannan yayi arba da wata siririyar gada
wacce farkonta wasu gumakan dodanni ne
akame.
kasan gadar kuma wutace takeci wani
lokacin ma.idanta lashi gadar sai wani taririn
hayaki ya tashi sama.
adaidai inda harisul mar,uf yake ga wani dan
karamin allon sanarwa an rubuta.
yakai bakon wannan daji ka sani .
wannan itace gadar da zata sadaka da abin
da kazo nema.dolene kabi ga kanta kaje
karshenta sannan zaka sami abinda kake
nema.
wadannan gumakan daka gani ba gumaka
bane dodannine bazasu taba mutuwaba face
kaje karshen wannan gada kadau abinda
kake nema.
yana gama karanta wannan allo sai ya
sakejin wannan iska ta sake zuko shi kasan
dajin baga ajiyeshi ako inaba sai bakin
wannan gada.tazarar dake tsakaninsa da iga
bata wuce taku dayaba.
kuma har awannan lokaci wadannan dodanni
suna cikin siffar gumaka.
kawai sai harisul mar'uf ya daga kafarsa ta
dama ya dorrta akan gadar kawai sai yaga
idanun wadannan dodanni ya bude,alamar
cewa ruhinsu ya soma dawowa.
batareda tsoroba ya sake dora kafarsa ta
hagu kan gadar.
nantake wata irin walkiya ta baiyana ta
haskake dajin baki daya dukda cewa ranace
ba dareba.
walkiyarna daukewa ruhin wadannan dodanni
ya dawo.
nan taki suka biyo harisul mar'uf
abaya,nanfa suka kasa tseren gudu dashi
domin su kamashi su hallakashi.
wohoho dan kaji ance ga k gudu to sa
gudune baizo ba.
ana fara wannan tseren gudune gadar da su
ke kai ta soma girgiza kamar zata karye.
bakomai ya janyo hakaba face tsananin

karfin takunsu.
saida suka wuce sa'a uku sannan suka iso tsakiyar gadar,inda nanne wutar tafi gasawa, nanfa tsananin zafi ya soma ruda harisul mar'uf inda matukar galabaitar dashi kenan hartakai cewa,baya iya gudu sosai.
cikin kankanin lokaci wadannan suka iso inda harisul ma'uf yake.
cikin shammace daya daga cikinsu yasa kafa yayi bal dashi.
sabo da karfin dukan sai dayayi sama kamar anjanyeshi da majajjawa ya tafi kamar zai fada cikin wutar amma sai ya wulkila jikinsa ya rike karfen da akayi gadar dashi. da hannunsa na dama sannan yadawo kan gadar akaci gaba da tseren gudun atsakaninsu.
a lokacinda wannan abu ke faruwa sai gadar ta fara girgiza tana neman tsinkewa.
koda dodannin suka lura da haka sai gaba dayansu sukayi tsalle suka sha gaban harisul mar'uf suna masu kaimasa duka da kafafunsu nantake kuwa suka rikirkita saboda tsananin zafin namansu,da kuma karfin damtsensu.
koda aka dau tsawon lokaci ana wannan artabu sai ya fuskanci.
tabbas idan aka dau tsawon lokaci ana wannan artabu tabbas zai iya hallaka.
koda yagama wannan tunani sai yayi yataka kan daya daga cikin dodannin cikin azababben gudu yadinga tafiya akan kawunansu harya isa kan na karshens.sanna ya sauka izuwa kan gadar yana tsala gudu fiye da farko saigashi awannan lokaci yayiwa dodannin mugun nisa.
sai bayan sa'a daya sannan ya fara hango wata yar karamar bishiya.adaidai kuma wannan lokaci gadar da suke kai ta tsinke..
cikin zafin nama harisul mar'uf wani itace da akayi gadar dashi ya dinga kamawa yana hawa sannan ya iso karshen gadar.
yannzuwa karshen gadar ne ya hango

dodannin sunyi wani irin tsalle suna kama
gadar.
koda ganin hakan sai harisul mar'uf yayi
tsalle ya haye kan wannan wannan bishiya
sannan ya tsinko wata ciyawa dake kana
bishiyar.
yan tsinkar ciyawar yaga duk gaba daya
dodannin sun kama da wuta sun kone
kurmus koda boka ulumanu yazo nan a labarinsa
saiyaga gaba daya hadiman sun nutsu suna
sauraronsa.
da ganin haka sai yayi dariya sannan yace
wannan shine takaitaccen tarihin harisul
mar'uf bayan bukata ta biya zan karasa
muku tarihin nasa.
yana gama wannan magana sai duk gaba
dayan hadiman sukai sujjada agareshi suna
masu cewa.
nasara ta tabbata agareka ya sarkin
matsafan duniya....
kafin sukarasa maganar tasu boka ulumanu
ya bace bat tamkar bai taba wanzuwa ba.
+++ ++++ ++++ ++++
wannan shine abinda ya faru afadar boka
ulumanu mai shirin mulkar duniya.
al'amarin yarima saiman kuwa alokacin da
suka kutsa kai izuwa cikin wannan daji sai
suka kasance cikin suna masu tsala
azababben gudu nagaban kwatance tamkar
zasu fita daga duniyar gaba daya.
basu tsaya da tafiyaba saida suka fuskanci
dare yayi sannan suka yada zango awani daji
mai matukar duhuwa.
a sannan ne yarima saiman ya umarci
dakarunsa dasu tsaya da tafiyar d suke.
nantake kuwa suka cika umarni.
wani badakare mai suna zamnal ya matsa
kusa da yarima saiman yace yashugabana ni
aganina bai kamata mu yada zango awannan
dajiba domin baza'a rasa mugayen namun
daji acikinsa ba.
dajin haka sai yarima saiman ya juyo ya dubi
zamnal yace

shin baka ganin muna tafiyane tare da
mata,yara da tsofaffiba?
kasani tafiyarmu dasu awannan yanayi yafi
hatsari akan zaman mu a wannan daji.
saboda haka ina umartarku dakuje ku kafa
mana tanti inyaso gobe da safe sai muci
gaba da tafiya.
dajin haka sai badakaren yace angama ya
shugabana.
sanna ya tafi ya umarci yan uwansa dasu
kafa tantunan da za'a kwana aciki.
sannan wasu kuyangi sukaje suka shirya
musu abincin da zasu ci.aka mikashi ga
kowanne tanti.
bayan angama shirya komai sai yarima
saiman yafito ya dubi dakarunsa yace
yaku yanuwana duka gaba dayanku kunsan
abindaya baro mu daga gida.
adalilin hakane na yanke hukuncin da nake
ganin shine zai amfanemu.wannan shawara
itace
ni banaso ko mutum daya daga cikinmu ya
mutu,domin yin hakan babbar asarace
agaremu.
shawara ta farko dazan baku itace kada daya
daga cikinku yace zai tayani fada da duk irin
abinda kukaga na hadu dashi.
shawara ta biyu itace
aduk inda kuke ku kasance kuna tare da juna
koda kuwa wani abin tsoron kuka
gani,muddin bagani kukayi zaku hallaka gaba
daya ba.
shawara ta uku itace
aduk inda muke kada mudinga yin barci gaba
dayan mu idan dare yayi,saidai midinga raba
dare.
aduk sanda wani ya nemi taimako to mu
taimaka masa koda bai kasance dan kabilar
mu ba.
idan mukayi riko da wannan shawara to
tabbas bukatarmu zata biya.
da wannan kalami nake muku bankwna sai
bayan wayewar gari zamuci gaba da tafiya.

da gama fadin haka sai ya wuce izuwa cikin tantinsa.
sannan suma ragowar tawagar suka tarwatse kowa ya koma abakin aikinsa.
bayan ya isa cikin tantinsa saiya tarar da gimbiya suhaila taci ado.ga wasu kuyangi guda biyu suna bata abinci abaki,biyu kuma suna yi mata tausa.
daganin sigowar yarima saiman sai wadannan kuyangisuka tashi suka fice daga turakar suka bar yarima da gimbiya suhaila kadai a zaune acikin tantin.
cikin farinciki gimbiya suhaila tace lale marhaban dababban masoyina na duniya.
nantake ta rugo da gudu ta rungume yarima saiman sannan
zo muje mu zauna yakaimijina domin tsawon wannan lokaci da muka dauka banganka ba ji nake tamkar shekara guda ce bamu haduba.
dajin haka sai yakama hannunta sukaje suka zauna akan wata shimfida mai taushi.
sannan yadubeta yace.
kamar yadda kika kasance haka nima nakasance domin dalilin halin dana shigane yasa nina umarci dakarunmu dasu dakata da tafiya.
haka kuma acikin tafiyata bana tunanin wahalar dake gabanmu muddin kina kusa dani.
yanzu haka muna cikin daji hayatul arzum akwai muggan dabbobin daji acikinsa kuma acikinsa zamu nemi hnayar zuwa dajin kurusul saudam.
dajin haka sai tace dashi hakane amma akwai wata matsala.
LIKE AND COMMENTS IS OUR  (IBNI ABDULLAHI ABDULLAHI)
LITTAFIN
BAKAR GABA PART 4
LBR
HABIBULLAH KBR
TYPING
HABIBULLAH KBR

koda boka ulumanu yazo nan a labarinsa
saiyaga gaba daya hadiman sun nutsu suna
sauraronsa.
da ganin haka sai yayi dariya sannan yace
wannan shine takaitaccen tarihin harisul
mar'uf bayan bukata ta biya zan karasa
muku tarihin nasa.
yana gama wannan magana sai duk gaba
dayan hadiman sukai sujjada agareshi suna
masu cewa.
nasara ta tabbata agareka ya sarkin
matsafan duniya....
kafin sukarasa maganar tasu boka ulumanu
ya bace bat tamkar bai taba wanzuwa ba.
+++ ++++ ++++ ++++
wannan shine abinda ya faru afadar boka
ulumanu mai shirin mulkar duniya.
al'amarin yarima saiman kuwa alokacin da
suka kutsa kai izuwa cikin wannan daji sai
suka kasance cikin suna masu tsala
azababben gudu nagaban kwatance tamkar
zasu fita daga duniyar gaba daya.
basu tsaya da tafiyaba saida suka fuskanci
dare yayi sannan suka yada zango awani daji
mai matukar duhuwa.
a sannan ne yarima saiman ya umarci
dakarunsa dasu tsaya da tafiyar d suke.
nantake kuwa suka cika umarni.
wani badakare mai suna zamnal ya matsa
kusa da yarima saiman yace yashugabana ni
aganina bai kamata mu yada zango awannan
dajiba domin baza'a rasa mugayen namun
daji acikinsa ba.
dajin haka sai yarima saiman ya juyo ya dubi
zamnal yace
shin baka ganin muna tafiyane tare da
mata,yara da tsofaffiba?
kasani tafiyarmu dasu awannan yanayi yafi
hatsari akan zaman mu a wannan daji.
saboda haka ina umartarku dakuje ku kafa
mana tanti inyaso gobe da safe sai muci
gaba da tafiya.
dajin haka sai badakaren yace angama ya

shugabana.
sanna ya tafi ya umarci yan uwansa dasu kafa tantunan da za'a kwana aciki.
sannan wasu kuyangi sukaje suka shirya musu abincin da zasu ci.aka mikashi ga kowanne tanti.
bayan angama shirya komai sai yarima saiman yafito ya dubi dakarunsa yace yaku yanuwana duka gaba dayanku kunsan abindaya baro mu daga gida.
adalilin hakane na yanke hukuncin da nake ganin shine zai amfanemu.wannan shawara itace
ni banaso ko mutum daya daga cikinmu ya mutu,domin yin hakan babbar asarace agaremu.
shawara ta farko dazan baku itace kada daya daga cikinku yace zai tayani fada da duk irin abinda kukaga na hadu dashi.
shawara ta biyu itace
aduk inda kuke ku kasance kuna tare da juna koda kuwa wani abin tsoron kuka gani,muddin bagani kukayi zaku hallaka gaba daya ba.
shawara ta uku itace
aduk inda muke kada mudinga yin barci gaba dayan mu idan dare yayi,saidai midinga raba dare.
aduk sanda wani ya nemi taimako to mu taimaka masa koda bai kasance dan kabilar mu ba.
idan mukayi riko da wannan shawara to tabbas bukatarmu zata biya.
da wannan kalami nake muku bankwna sai bayan wayewar gari zamuci gaba da tafiya.
da gama fadin haka sai ya wuce izuwa cikin tantinsa.
sannan suma ragowar tawagar suka tarwatse kowa ya koma abakin aikinsa.
bayan ya isa cikin tantinsa saiya tarar da gimbiya suhaila taci ado.ga wasu kuyangi guda biyu suna bata abinci abaki,biyu kuma suna yi mata tausa.

daganin sigowar yarima saiman sai
wadannan kuyangisuka tashi suka fice daga
turakar suka bar yarima da gimbiya suhaila
kadai a zaune acikin tantin.
cikin farinciki gimbiya suhaila tace lale
marhaban dababban masoyina na duniya.
nantake ta rugo da gudu ta rungume yarima
saiman sannan
zo muje mu zauna yakaimijina domin tsawon
wannan lokaci da muka dauka banganka ba
ji nake tamkar shekara guda ce bamu
haduba.
dajin haka sai yakama hannunta sukaje suka
zauna akan wata shimfida mai taushi.
sannan yadubeta yace.
kamar yadda kika kasance haka nima
nakasance domin dalilin halin dana shigane
yasa nina umarci dakarunmu dasu dakata da
tafiya.
haka kuma acikin tafiyata bana tunanin
wahalar dake gabanmu muddin kina kusa
dani.
yanzu haka muna cikin daji hayatul arzum
akwai muggan dabbobin daji acikinsa kuma
acikinsa zamu nemi hnayar zuwa dajin
kurusul saudam.
dajin haka sai tace dashi hakane amma
akwai wata matsala. cikin tsananin mamaki yadubeta yace
me kike nufi ?
gimbiya suhaila tace idan muka fiya yada
zango to hakan zai baiwa magauta dama
akan mu
shin baka tunanin cewa akwai wata sabuwar
masifar da take shirin fadomana bayan ta
boka ulumanu ?
kodajin haka sai hankalin yarima saiman ya
tashi yaji gaba daya zuciyarsa ta dugunzuma
nantake ya nuna bangon tantin nasu da
yatsansa na hannu
faruwar hakan keda wuya saiga hoton fadar
boka ulumanu ta baiyana tundaga lokacin da
sukayi walimar farko afada ,har izuwa
lokacinda ya aiki aljani markazulu ya kashe

dodo sharmanu da yarsa .
koda sukazo daidainan sai hoton komai ya dauke tamkar baitaba wanzuwaba.
da ganin haka sai gimbiya suhaila ta dubeshi tace to wannan abu daya faru bakaramin tashin hankali bane anahiyar nan baki dayaba ,domin dodo garjaju bazai taba hakuriba akan wannan abu daya faruba .
kodajin haka sai yarima saiman yabushe da dariya sannan yace .
nafiki sanin kowaye garjaju don haka kafin muje inda yake zansan hanyar da zamubi mu hallakashi farat daya
nantake ya tashi yaja hannun gimbiya suhaila izuwa kan wanish luntsumemen gado suka kwanta .
kwanciyarsu keda wuya sai bacci ya daukesu acikin tantin.
acan sansanin dakarun su yarima saiman Kuwa sai raba kwanciya kamar yadda ya tsara musu suka raba kansu gida biyu kaso nafarko suka fara kwanciya sannan kaso nabiyu suka kwanta
kash hakika rashin sani yafi dare duhu ashe awannan wuri da suka yada sansani akwai wasu mugga muggan yanfashi amma su akaidarsu basayin fashi acikin dare sai da asuba ta doso kai sannan suke farawa zuwa faduwar rana .
wannan daliline yasa basu kawowa su yarima hariba tun sanda shigo dajin.
amma kuma tundaga shigowar su yarima sai suka fara haka tarkuna yadda zasu kashesu farat daya .
acikin tantin yarima Kuwa lokacin da suka nutsa cikin barci .gimbiya tayi wani mafarki inda ta hangi wasu kananan karnuka akan hanyarsu suna kokarin yi musu kisan farat daya .
koda daidainan amafarkin nata saita farka afirgice,tasa hannu tatashi yarima .
cikin firgice tadubi yarima tace yakai masoyina kayi hakuri bisa tashinka daga

barci da nayi .
hakan ta farune sakamakon wani mummunan mafarki da nayi .tun ina yarinya idan nayi mafarki yana zama gaskiya ba'a taba samun akasiba
to a darennan nayi mafarki inda aka nunamini wasu muggan yanfashi akewaye damu suna dana mana tarkunan mugunta.idan har bamu dauki matakiba to tabbas zamuyi asarar rayuka da yawa .
kodajin sai ya dubeta yace madallah da mata tagari hakika ina matukarjin dadi da irin taimakon dakike bani
nantake ya tashi yafita daga cikin tantin nasa ya nufi inda dakarunsa suke,koda sukaga yarima sai suka durkusa cikin girmamawa.yarima ya dubesu yace
akwai wani abu dake shirin faruwa idan har bamu dauki matakin gaggawa ba
shawarar dazan baku itace dakunga alfijir yafara fitowa kusami kibiyoyinku,kusaita hanya guda daya daidai inda tarkon yake saiku harbata,to dazarar kunyi haka tarkunan abokan gaba zasu lalace.gurin da aka birnine tarkunan Kuwa yana nan gaba damu daga barin gabas tafiyar rabin sa'a idan har muka sami nasarar lalata tarkunan to zamu sami nasarar fita daga san saninmu lafiya
nine kadadai wanda zai taresu da yaki da zarar munyi gaba da gaba dasu.kukuma saiku zama yan kallo .
ku aikinku shine bawa jama'armu tsaro.idan mukayi haka to zamu sami nasara akansu .
haka suka kasance cikin wannan halin hr izuwa lokacin da alfijir yafara ketowa nan take Kuwa dakarun suka Debo kibiyoyi suka dana ajinkin baka sannan suka sukayi tafiyar rabin sa'a.sannan suka saita gabansu kadan suka harba kibiyoyin,kwatsam saiga wasu muggan tarkuna suna fitowa daga karkashin kasa masu matukar hatsari ga rayuwar dan adam.
faruwar hakan keda wuya saiga wasu

muggan yanfashi suna fitowa daga cikin
maboyarsu suna masu karji gami da kuwwa
nufo su yarima saiman .
koda ya rage baifi saura taku gomaba
tsakaninsu da sansanin sai yarima saiman
yafito cikin muguwar shigar yaki .
nantake yasa kafa yadoki wasu dakaru dake
gabansa .saboda karfin dukan saida sukai
tsalle suka gwaru da wata bishiya .nantake
kashin bayansu ya karye .
cikin karaji ya hausu da sara da suka tako
ina sai ga kawunan bila'adama yana yawo a
sararin samaniya .
jini Kuwa yadinga yawo kamar anbude
idaniyar ruwa .
sassan yadinga yawo kamar ana sassabe
agona .
sai gashi mutun daya ya zamewa mutane
dubunnai alakakai tamkar guguwar zame masu guguwar annoba.su kansu
sunsan cewa yau sun hadu da gamonsu rana
ta baci domin basu taba haduwa da wani
jarumi ba kwatankwacin sa.domin fada
yakeyi tamkar ba jikin jini da tsokane da
shiba.
kafin cikar sa'a biyu ya karar da rabinsu.
koda shugaban yan fashin ya lura da abin
dake faruwa,sai ya daka musu tsawa.
nan take kuwa suka dakata da fadan.
shugaban nasu ya matso inda yarima yake ya
tsaya agabansa,sai ga yarima saiman ya
zamo dan kankani agabansa.
shugaban nasu ya dubi yarima yace
tabbas jarumtakarka ta burgeni don haka ina
gayyatarka daka shigo cikin kungiyarmu,zan
baka babban mukami idan kayarda.
idan kuwa kaki ni da kaina zan kasheka.
koda jin haka sai yarima ya daka masa
tsawa yace
kai lalataccen banza kune kuka bata mana
nahiya da kashe kashen rayukan wadanda
basu jiba basu ganiba.
don haka nadau alkawarin ganin bayanku
babu wani sulhu a tsakaninmu.

da gama fadin haka sai ya afka masa suka kachame da azababben yaki fiye dana farko.
ya zamana suna kaiwa junansu sara da suka cikin kwarewa.sai gashi yarima yazama dan karami agaban wannan dan fashi amma abinda zai baka mamaki shine.
a fannin iya yaki yarima ya tattaka dan fashin.
wohoho hakika jarumtaka baiwace wanda allah ya baiwa ya huta
duk da tsananin karfi irin na wannan dan fashi sai ya zama na banza domin kokarin kare kansa yake yana neman hanyar tsara.
koda yarima ya fuskanci nufin wannan dan fashi sai ya shammace shi yasa takobi ya sare masa kai.
nantake gangar jikin ta fadi kasa.
koda raguwar yan fashin sukaga gawar shugabansu akasa .sai duk suka zubar da makamansu suka ruga da gudu.
nanfa yarima saiman ya dinga bin dakarun daya bayan daya yana kashesu har sai da ya karar dasu gaba daya sannan ya dawo wajen sansaninsu.
da isowarsa sai ya tarar da dakarunsa da jama'arsa suna ihun farinciki. a gaban dakarun kuwa babu kowa sai gimbiya suhaila.
tayi shigar wata jar riga mai tsananin kyau.ta daure gashin kanta agadon bayanta sai sheki da walwali yakeyi.
cikin murna ta jawo hannun yarima saiman izuwa cikin tantinsu,sannan ta dauko wani daddadan abinci ta ajiye masa.
nantake kuwa ya faracin abincin cikin nishadi da annashuwa.
da gamawarsa saita dubeshi tace ina tayaka farin cikin samun nasararka a wannan yaki.
ya dubeta yace nayi wannan aikine domin kare mutuncin al'ummarmu.
don haka yanzu zamu tashi mubar wannan guri muci gaba da tafiya don biyan bukatarmu.

yana daga cikin tantin nasa yakira shugaban dakarunsa mai suna zamnal.
cikin kankanin lokaci shugaban dakarunya iso cikin tantim dare da fadin gani ya shugabana.
yarima yadube shi yace inaso ka umarci dakarunmu dasu gaggauta hada kayansu don muci gaba da tafiya.zamnal yace angama ya shugabana.
nantake zamnal ya tashi ya fice daga cikin tantin nasu.
cikin kankanin lokaci kuwa suka hada inasu inasu suka cigaba da tafiya izuwa hanyar da zata kaisu dajin kurusul saudam saida suka shafe lokuta masu tsawo suna tafiya sannan suka iso wata mararrabar hanya wacce ta kasu kaso hudu.
nantake sukaja birki suka tsaya sukayi cirko cirko cikin rashin sanin hanyar da yakamata subi
ana cikin wannan hali sai yarima saiman ya tuna da maganar da mahaifinsa yayi masa akan zoben hannusa.
koda gama wannan tunani sai ya zaro zoben daga hannunsa sannan ya murza.
faruwar hakan keda wuya sai wani haske ya fito daga jikin zoben ya nuna musu hanyar data nufi yammcin dajin.
inda yake musu nuni da cewa itace hanyar dajin kurusul saudam.
koda ganin haka sai yarima saiman ya juyar da linzamin dokinsa zuwa hanyar da hasken ya nufa.cikin tsala azababben gudu.
WANNAN SHINE ABIN DAYA FARU GA YARIMA SAIMAN AKAN HANYARSU TA ZUWA DAJIN KURUSUL SAUDAM
++ +++ ++
Al'amarin aljani karkazulu kuwa lokcin daya bar kogon daya kashe samriya da babanta kuwa.
sai ya kasance yana tsala gudu nagaban kwatance asararin samaniya ba tare da sanin inda zaijeba.cikin jin izza da takama.

yana cikin tafiyarne ya fara tunane tunane
akan wanne shiri yakamata yayiwa kansa.
tabbas yanada bukatar karawa kansa shiri ta
yadda zai iya hallaka boka ulumanu cikin
sauki batare da wata wahalaba.
sannan kuma ya tuna da batun dodo garjaju
yanzu yana cikin fushi dashi.
yana cikin wannan tunanine kuma ya tuno da
batun yarima saiman.
i dan hada kai dashi to tabbas zai sami
nasara.sannan kuma bayan bukatarsa ta
tsira sai ya yaudari yarima saiman ya
hallakashi.
koda gama wannan tunani sai ya bushe da
dariyar mugunta.
sannan ya juya ya nufi hanyar dajin kurusul
saudam (IBNI ABDULLAHI ABDULLAHI)
LITTAFIN BAKAR GABA
PART 5
LBR
HABIBULLAH KBR
TYPING
HABIBULLAH KBR
koda sarki abu saiman yazo nan azancensa
sai mutane suka kamu da murna har sunayi
masa jinjina
da kirari tamkar suna da tabbacin samun
nasara awannan yaki
koda ganin haka sai farinciki ya kamashi
sannan yace
daga wannan rana inason makeran dake
cikin birnin nan da su dage wajen kera
miyagun makaman yaki
wadanda zamuyi amfani dasu awannan yaki.
sannan mayakan mu su dage wajen baiwa
kansu horon yaki tare da sauran mutanen
gari
sannnan duk wanda yakasance yana da ilimi
wajen sanin tarkunan yaki ina nemansa
yanzu a tsakiyar fada
yana gama fadin haka sai dakaru suka dare
sai ga wani dattijo yafito fuskarsa cike da
furfura

amma da kaganshi kasan y asaba da
kwarmatsuw a filin daga.
sannan wasu samari guda biyu suka fito
daga cikin jama'ar gari suma suka tsaya
akusa da wannan dattijo.
dukkansu suka rissina agaban sarki.
dattijon ya rissina ga sarki sannan yace
ni sunana zamnur kuma ina daga cikin
manyan dakarun wannan birni
kuma ina da ilimi na musamman wanda na
koya a makarantar horon yaki tun ina
matashi.
dajin haka sai sarki yace
to wacce irin shawara zaka bamu game da
wannan yaki?
dattijon yace ina da wasu tarkuna wadanda
nake ganin zasu taimaka mana a wannan
yaki
sudai wadannan makamai bakomai bane face
wasu kananan allurai
wadanda ake daurasu asaman bishiyoyi.
dazarar abokan gaba sun iso sai a tura
dakaru kamar guda ashirin su watso
wadannan allurai
da zarar anyi haka zasu cake ajikin abokan
gaba ba tare da sun lura ba
saboda tsabar kankantar su.
saidai daga baya dakarun zasu dinga fadowa
daga kan ababan hawansu matattu
koda jin haka sai sarki abu saiman yayi
murmuashi yace
tabbas wannan dabara taka tayi dai dai don
haka zanuyi amfani da ita.
sannan saurayi na biyu yafito ya tsaya gaban
sarki yace
ni sunana ruslan da ga sarkin dajin wannan
birni
mu a gidan mu akwai sihirin tsafin da
mahaifin mu yabar mana na wadansu
kunamai maau fuka fukai wadannan kunamai
suna nan a cikin dajijjikan dake kewaye da
birnin nan
mahaifin mu a bincikensa ya gano da akwai

wadannan kunamai
sannan ya boyesu da karfin sihirinsa.
kafin ya mutu saida ya barmana turaren da za'aje akunna shi acikin daya daga cikin dajijjikan wannan kasa.
da zarar anyi haka bayan sa'a uku wadannan kunamai zasu baiyana su cigaba da aikin su na tsaron wannan birni.
koda ya gama fadin haka sai ya koma kusa da tsoho zamnur ya tsaya.
sai saurayi na uku shima ya fito gaban sarki ya tsaya yace
nine sadauki huskan masanin taswirar dajijjikan dake wannan kasa.
sannan nasan wadansu tarkuna da ake binne su a karkashin kasa.
sudai wadannan tarkuna za'a hadasune da wani sinadarin magani wanda ake jikashi acikin sanan a sami manyan tuluna azubashi aciki
sannan a sami igiyoyi adaure tulunan dasu.
bayan anyi haka sai asami wasu dakaru su hau saman bishiyoyi da zarar abokan gaba sun iso sai suja wadannan igiyoyi.
nantake tulunan zasu watsawa maykan ruwan dake cikin tulun.
da zarar ruwan ya taba jikinsu
nantake jinin jikinsu zai kafe su zama gawarwaki.
koda wadannan mazaje suka gama fadar fasahar su sai sarki abu saiman ya bushe da dariya
sannan yace
tabbas kun bada shawara mai kyau,da kuma babbar gudun mawa
don haka zamuyi amfani da ita.
nan take ya sallami jama'ar gari baki dayansu sannan sannan ya shige cikin gidan sarauta
WANNAN SHINE ABINDAYA FARU ABIRNIN RAMLATUL SAIF BAYAN SARKI ABU SAIMAN YA HADA ZAMAN FADA
++ ++ ++

al'amarin yarima saiman kuwa lokacin da
suka durfafi dajin kurusul saudam kuwa
sai suka kasance cikin tsala azababben gudu
saida suka shafe kwana goma suna tafiya
sannan suka iso dajin kurusul saudam
suna isowa sukayi arba da wasu dogayen
bishiyoyi wadanda sai an daga kai sannan
ake ganin karshensu
suna isowa daidai wannan guri sai yarima
saiman yaja linzamin dokinsa ya tsaya cak
sannan jama'ar dake bayansa suma suka ja
nasu linzaman dawakan.
yarima saiman ya juyo ya dubesu yace
wannan shine farkon dajin kurusul saudam
don haka nanne gurin da zamu rabu daku
nina tafi izuwa naman takobin sihiri
bana bukatar taimakon kowa daga cikin ku
har naje na dawo.
taimako daya kurum nake nema agurinku.
shine ku kula da lafiyar gimbiya suhaila har
izuwa lokacin da zan dawo.
koda gama fadin haka sai yarima yaga
zamnal jikinsa yayi sanyi
kawai sai yaji tausayinsa ya kamashi.
nantake ya matso kusa dashi yace.
kayi hakuri ka zauna kusa da jama'ata bana
son arasa ko mutun daya daga cikin ku.
don haka nake kokarin hanaku shiga cikin
abubuwa masu hatsari.
yana gama fadin haka sai ya nuna jama'arsa
da hannunsa
nantake wata raga mai kamar kejin karfe ta
fito daga cikin hannunsa ta kewaye su yadda
babu wanda zai iya fitowa daga cikinsu.
sannan yace dasu daga yanzu babu wani
hatsari dazai sameku har naje na dawo
yana gama fadin haka haka sai ya juya da
nufin ya shiga cikin dajin kwatsam sai yarima saiman yaga sararin
samaniya tayi duhu.
kawai sai ga aljani markazulu ya baiyana a
saman kan yarima saiman.
nan danan aljanin ya sauka a gaban yarima
sainan

nanfa aka soma kallon kallo atsakaninsu na
tsawon lokuta
sanan yarima saiman ya dubi markazulu
yace
kai kuma me ya kawo ka wannan dajin?
kodajin haka sai markazulu yace
nine markazulu tsohon hadimin boka
ulumanu
nazo gurinka ne don na nemi hadin kanka
mu yaki boka ulumanu.
kodajin haka sai yarima saiman ya turbune
fuska
sannan yace dashi
bana bukatar taimakonka har abada don
haka nan ne wajen daya kamata mu rabu
dakai.
bana bukatar na sake haduwa dakai nan
gaba domin bazatayi kyauba.
yana gama fadin haka sai ya kada linzamin
dokinsa ya shige cikin dajin yabar markazulu
atsaye.
nan take ya bace bat tamkar bai taba
wanzuwab.
shikuma yarima saiman kutsa kai cikin dajin
cikin gaggawa.
a wannan lokaci zuciyarsa cike take da
zumudin isa tsakiyar wannan daji don biyan
bukatarsa.
sai daya shafe sa'a shida yana tafiya acikin
dajin sannan ya iso karshensa tun daga nesa
ya dinga ganin dake cikinsa wasu irin many
manya
kirar mutanen farko
jikinsu amurde yake tamkar sassaka su akayi
da itace.
fuskokinsu cike suke da gashi kai kace
gwaggwan birine
suna da jajjayen idanuwa tamkar angasa dan
buda awuta.
koda suka lura da tahowar yarima saiman
sai daya daga cikinsu ya zaro wani kahon
giwa ya busa
nan take wata kara ta cika dajin gaba daya

tare da amsa kuwwa.
nan dan ragowar dakarun dake dajin suka lura da abin da yake faruwa
nantake suka ruga da gudu suka soma debo makaman yakinsu domin tunkarar yarima saiman.
sudai wadannan arnan dajin sunada matukar yawa domin zasu kai su dubu goma.
sannan suna karkashin mulkin wani hatsabibin matsafi wanda yake shugabantarsu.
kuma yasan dalilin zuwan yarima saiman don haka yasananr da ragowar dakarunsu don su san da zuwansa
yarima saiman yana isa kusa da inda dakarun suke sai yaja linzamin dokinsa ya tsaya cak
sannan ya budi baki yace
ku ma'abota rayuwar daji kananun jarumai wadanda suke tsoron rayuwa da mutane yan uwansu tamkar dabbobi
to yau ni saiman na zo wannan birni domin na yakeku na zubar da jininku na hana zuluncin da kukeyi adoron kasa da kwacen da kukeyiwa matafiya akan hanyarsu.
nayi alkawarin saina hallakar daku muddin bazaku yarda da sharadin danazo muku dashiba.
sharadin kuwa shine
inaso ku mikomini takibin sihirin da kuke bautawa cikin ruwansanyi domin mu rabu lafiya daku batare da an zubar da jini ba…
kafin ygama fadar maganar dake bakinsa sai su shugaban wadannan arnan daji yafito asukwane bisa wani ingarman doki ya tsaya agaban dakarunsa.
sannan ya bushe da dariya
ya dubi yarima saiman yace lallai kayi kuskure da kake tunanin zaka kwaci maigirma takobin sihiri a hannunmu.
inaso kasani cewa koda mutanen duniyane zasu taru basu isaba balle kai mutum daya tak

yana zuwa nan a zancensa sai ya umarci
arnan dajin dasu harbowa yarima saiman
kibiyoyinsu
nantake kuwa suka dana baka sukaharbo
masa .
saiga sararin samaniya tacika da kibiyoyi
sannan suka durfafo kan yariman saiman
nantake yarima saimanya zare takobinsa.
sannan yasawani silken sihiri ya lullube
dokinsa da ita gaba daya
sanna ya shiga kade kibiyoyin da suke harbo
masa cikin zafin nama,juriya da bajinta.
wohoho hakika jarumtaka baiwace duk
wabda allah yabaiwa ya huta.
wani abin mamaki shine gani yadda yarima
saiman yake kare hare haren da kibiyoyin
suke kawo masa cikin kankanin lokaci.
sai gashi anrasa kibiya ko guda daya wacce
zatq iya lakutar jikinsa.
sai bayan yan dakiku sannan kibiyoyin suka
kare.
nan fa dakarun suka rufo kansa aka kachame
da azababben yaki nagaban kwatance.
idan kaji ance ga ki gudu to sa gudu ne bai
zoba.
domin duk da karfin damtse irin na
wadannan dakru sai yarima saiman shi kadai
ya gagaresu suka rasa yadda zasuyi dashi.
domin yana wata jarumtaka ne taban al'ajabi
wacce na tsaya fasaltamaka itama bata
lokaci ne domin duk kwatancen mai kwatace
bai isa ya fasalta maka irin yaki da yakeyi
ba.
awannan lokaci kasa ta soma girgiza,kura ta
turnuke sararin samaniya saboda
kwarmatsuwar da suke yi akan kasa.
karar karafa ta cika dodon kunne,tare daihun
mazaje,jini ya dinga fallatsi akan kasa
tamkar an bude magudanar ruwa
awannan lokaci sabodane saboda tsananin
bala'i tsuntsaye suka dinga tashi suna
chanza sheka.
barewa suka dinga fadawa garken zakuna

basu sani ba don su ceci ransu.
duk inda yarima saiman yasa gaba saidai
kaga mazaje suna zubewa kasa tamkar ana
sassabe agona.
duk da irin wannan mummunar barna da
yake musu batasa sunja da bayaba.saboda
tsananin naci tamkar basu ake kashewaba.
sai wani irin karaji sukeyi suna dada kunno
kai cikin rashin tsoro da yarda dakai.
shi kuwa ya wanzu yana mai zare musu
ruhin numfashinsu tamkar mala'ikan mutuwa Sai da suka shafe sa'a uku suna fafat
wannan kazamin yaki tsakanin arnan dajin da
yarima saiman.
an rasa wanda zai sami galaba akansa
ana cikin wannan haline yarima saiman yaji
an gabza masa naushi da kafa agadon baya
saboda karfin naushin sai da yarima saiman
yayi tsalle kamar an janye shi da majaujawa.
kamar zai fadi kasa amma saboda tsananin
jarumtaka sai yarima saiman ya juya jikinsa
a sararin samaniya
sannan ya dire bisa kafafunsa.
amma kafin ya dawo cikin haiyyacinsa sai ya
sake jin an kara gabza masa wani sabon
naushin a kirji wanda yafi na farko.
saboda karfin naushin sai da yaji kamar
kashushuwan kirjinsa sun kakkarye.
bakowa ne yayi masa wannan duka face
shugaban wadannan arnan daji.
nan take ya takarkare ya bushe da dariyar
farinciki sannan ya dubi yarima saiman yace
lallai ka cika mai tsautsayin wahala tunda
har kake shirin raba mu da takobin sihirin
mu
yanzu kai a haka zakaje ka yaki dodo garjaju
har ka sami tsumin tsafinsa.
sannan kaje fadar sarkin aljanu ka rabasu da
miftahul darul sihir?
hakika yanzu zaka hallaka sannan naje na
kama ragowar mutanen da suke tare da kai
namai dasu bayin mu.
yana zuwa daidai nan a zanncensa saiya
zare takobinsa ya nufo kan yarima saiman da

nufin tsige masa kai.
ba zato ba tsammani sai yaji wata irin iska
mai karfi ta taso ta shureshi ta damfara shi
da kasa
bakowa bane yayi wannan aikiba face aljani
markazulu
nan take ya tashi yarima saiman zaune yace
kai jeka ka tari shugaban yan fashin
ni kuma zanje na tari ragowar dakarun in
yaso idan na gama dasu sai in taimakama.
yana zuwa daidainan azancensa sai ya shige
cikin dakarun ya hausu da sara da suka ta
ko ina babu kakkautawa duka inda ya nufa
saidai kaga arnan dajin na zuba a kasa
tamkar ana sassabe agona.
shi kuwa yarima saiman sai ya gyara rukon
takobinsa
ya nufi inda shugaban arnan dajin yake kai
tsaye.
nan fa aka soma kallon kallo a tsakaninsu
kai da gani kasan kar ce ta san kar.
har na tsawon dakiku daga chan sai suka ja
da baya kamar tazarar taku goma
atsakaninsu.
sannan suka gyara rukon takobinsu
suka rugo kan juna suka kacame da
azababben yaki mai matukar muni fiye da
wanda akeyi tsakanin aljani markazulu da
ragowar dakarun arnan dajin.
sai fadan nasu ya zamo abin tsoro kuma
abin sha'awa sakamakon yadda suke fadanda
dukkan karfin su.
shidai shugaban wadannan arnan daji wani
irin gabjejen mutum ne mai kirar muatanen
farko
sannan yana da manya manyan idanu jajaye
masu matukar kwarjini.
kirjijsa faffada ne cike da gashi.sai kace
zaki.
yana da manya manyan damatsa kamar
jerasu akayi.
kai duk inda mutum mai suffar karfi yakai to
wannan mutum yafishi cika ido

shi kuwa yarima saiman sai ya zama dan
karami akansa.
amma duk da haka sai gashi ya kasa samun
nasara akan yarima saiman saboda matukar
karfin damtsensa.
dajuriyarsa da kuma nacinsa.
hakika yarima saiman ya isa a jinjina masa
ganin yadda yake yaki da mutumin da ya
fisyi kwarjin da cika idanu.
dukkansu suna yi fadanne cikin mugun nufi
da burin salwantar da rayukan juna.
koda suka dau wani lokaci suna wannan
fafatawa .
sai dukkansu suka ja da baya.
suna hararar juna kamar zakaru.
daga chan suka sake falfalowa da gudu suka
sake kachamewa azababben yaki fiye da
farko.
sai gashi suna hadawa da sara da suka
sama da kasa.
har tsalle sukeyi suna kai farmaki ko kuma
wani lokacin kaga suna zamiya akasa.
awannan karon ma sai aka kasa samun
wanda zai nasara daga chan sai shugaban
arnan dajin yayi wurgi da takobinsa.
sannan yace da yarima saiman
tunda dai munga salon fadan namu iri
dayane to mai zai hana mu gwada karfin
damtsen mu banbance tsakanin aya da
tsakuwa.
kodajin haka sai yarima saiman yayi
murmushin yadda dakai sannan yayi wulli da
takobinsa.
nan take suka kachame da kokawa.
awannan lokaci sai fadan nasu ya chanja
salo domin ana fara fadanne kowanne daga
cikinsu jikinsa ya fara gaya masa.
duk sa'adda yarima saiman ya sami nasarar
dukan shugaban yan fashin sai kaga shima
ya rama kamar dama chan sun tsara haka
fadan zai kasance.
ana cikin haka yarima saiman yaga idan
suka ci gaba da fadan ahaka to zasu iya yi

ragas.
kawai sai ya shammaci shugaban arnan dajin ya yi tsalle ya kama kansa ya murde sannan ya wullar da gawarsa gefe daya.
koda ragowar arnan dajinsuka ga gawar shugabansu a kasa sai suka zubar da makamansu.
suka ruga da gudu nan take yarima saiman ya tashi ya dinga taimakawa markazulu suka dinga binsu suna rafkewa.
kafin cikar wasu yan dakiku sun gana hallakasu.
koda suka karar dasu sai yarima saiman ya juyo ya dubi markazilu sannan yace .
wai kai meyasa kake bibiyata ne shin ban hanaka biyoni ba?
kodajin wannan tambaya sai markazulu yace kayi hakuri yakai wannan jarumin jarumai bana biyo ka bane don na cuce ka ba.
na biyo kane kawai don nasan ra'ayin mu daya dani dakai ma'ana na yakar boka ulumanu.
kodajin haka sai yarima ya sake tambayar sa yace to menene dalilin da yas a kake da burin yakarsa?
kodajin wannan tambaya sai aljani markazulu yayi shiru kamar bazaice komi ba.
daga chan sai yace
mun sami sabani da uban gidanane sakamakon nima na sami babban matsayi a fannin sihir.
koda gama jin haka sai yarima saiman jinjina kansa azuciyarsa yace tabbas akwai wani boyayyan sirri a zuciyar markazulu.
don haka dolene nasa idanu aknsa.
kawai sai yace da markazulu.
shikenan na amince da tafiya tare da kai.
amma da sharadi.
sharadin kuwa shine bazakaci amanarmu ba.
kodajin haka sai markazulu yace na amince da wannan sharadi naka.
nan take suka kama hanya suka shiga cikin garin arnan dajin.

sai da suka wuce sa'a biyu sannan suka iso
kofar wani babbar fada..
Suleiman Zidane kd
Whatsapp. 08161272634

LIKE AND COMMENTS IS OUR ENCOURAGEME
DOMIN SAMUN CIGABAN SAI KU KASANCE DA MU A KODA YAUSHE
DAGA
Suleiman Zidane kd
Whatsapp. 08161272634